## NTA TARE DA AREWA24 ZA SU FARA HADIN GWIWA KAN SHIRYE-SHIRYENSU

**April 12, 2016** – Hukumar Talabijin ta Najeriya (NTA) da AREWA24, tashar tauraron Dan-Adam da take yada shirye-shiryenta masu nishadantaarwa da kayatarwa a harshen Hausa, na sanar da hadin gwiwar yada shirye-shirye da ya hada da daukacin tashoshin NTA 17 da suke watsa shirye-shiryensu a Arewacin Najeriya. A karkashin wannan yarjejeniya mai dimbin tarihi, tashoshin NTA na Arewacin Najeriya zasu fara watsa wasu zababbun shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta kuma wadanda suka fi karbuwa, da suka hada da shirin wasan kwaikwayon da ya sami lambar yabo wato, "Dadin Kowa," da kuma wasu shirye-shiryen guda hudu. NTA da AREWA24 ra'ayinsu yazo daya wajen samarwa masu kallo a Arewacin Najeriya shirye-shiryen da suka karbu, kuma suka dace da al'adunsu, masu inganci da nishadantarwa. Tashoshin NTA na farko sun hada da: NTA-Abuja, NTA-Bauchi, NTA-Kaduna, NTA-Kano, NTA-Maiduguri da NTA-Sokoto, da kuma wasu sababbin tashoshin da za'a bude watanni masu zuwa.

A cewar Maxwell Loko, Managing Director, NTA Television Enterprises, "Wannan sabuwar hadin gwiwar da AREWA24 zata bawa tashoshin NTA na Arewacin Najeriya damar sadar da masu kallon su da ingantattun shirye-shirye na ainihi masu kayatarwa kala daban-daban."

Bayan Dadin Kowa, shirye-shiryen AREWA24 da za'a rika nunawa a tshoshin NTA sun hada da "Kundin Kannywood," shirin bayan fage na masana;antar Kannywood, jarumai, masu bada umarni da masu fada aji; "Alawar Yara," shiri ne na yara; "Matasa@360," shiri ne a kowane sati da yake tsokaci akan al'adu da rayuwar matasan Arewacin Najeriya da suka fito daga fanni daban-daban; "Waiwaye," shiri ne da yake tsokaci akan al'adu da kirkire-kirkire; "Tauraruwa," tambihi ne akan mata kallabi tsakanin rawuna daga fanni daban-daban; da kuma, "Zafafa Goma" (Top-10), shirin tashar na kade-kade da fitaccen mawakin Hip Hop na AREWA24 Nomiis Gee, ke gabatarwa.

"AREWA24 na farin cikin aiki tare da NTA wajen bawa NTA shirye-shiryenmu da suka fi kyau domin masu kallo a Arewacin Najeriya," Manajan daukakawa da bunkasa tashar AREWA24, Kabiru Riruwai wanda yake gudanar da wannan hadin gwiwar ta bangaren AREWA24 yayi nuni da cewa. "Duba ga yadda NTA ta mamaye ko ina da kuma tsohon tarihin da take da shi a dukkan fadin kasar nan, wannan hadin gwiwar zai bawa 'yan Arewaacin Najeriya daga kowane sashi na rayuwa damar samun ingantattun shirye-shiryen da suka dace da al'adar Hausa," inji Riruwai.

Celestine Umeibe, shugaban sashin tallace-tallace na AREWA24, ya kara da cewa, "Wannan hadin gwiwar da NTA nasara ce karara ga kowane bangare wanda ya zama dai dai da bukatunmu na bunkasa harkokin kafafen yada labarai a Arewacin Najeriya."

AREWA24 a yanzu tana da shirye-shirye na kashin kanta guda 13 a tashar ta da ke Kano, wadanda suka hada da Dadin Kowa, shirin Karin kumallo a kowace safiya, Kundin Kannywood, Waiwaye, Matassa@360, Alawar Yara da Tauraruwa (Role Models); da kuma tagwayen shirin kade-kade, H Hip Hop da Top 10. Sauran shirye-shiryen sun hada da, Taka Leda, shirin da yafi kowanne a fannin wasanni da kuma Daga Masa Kallon Mu, da shirin girke-girke.

Kano, Nigeria — The AREWA24 Channel, LLC — Lagos, Nigeria
www.arewa24.com
info@arewa24.com
+234-802-367-3730

**Game da NTA**: Burin NTA shine ta mallaka, ta habaka, sannan kuma ta daga darajar kyawawan dabi'un Najeriya ta hanyar shirye-shiryen da suka kunshi, al'adu, siyasa, tattalin arziki; ta zama turba ta wayar da kai ta hanyar ilimantarwa, fadakarwa da kuma nishadantarwa; sannan kuma ta killace al'adun Najeriya ta kuma habaka fahimtar al'adu da siyasa a Najeriya da kuma ketare. A yau, NTA (www.nta.ng) na alfaharin tashoshi 101 bayan daukar matsaya da gwamnatin tarayyar Najeriya ta yi a shekarar 2002 ta kara habaka samar da tashoshin talabijin, musamman a karkara. Wannan cigaba da aka samu ne yasa NTA ta zama a matsayin da babu kamarta a Afirka.

**Game da AREWA24:** AREWA24 (arewa24.com) it ace tashar tauraron Dan-Adam kwaya daya tilo mai watsa shirye-shiryenta 24/7 a cikin harshen Hausa na kashin kanta, kuma akan al'amuran Arewacin Najeriya, al'adu, matasa, kasuwanci, kirkire-kirkire da kuma nishadantar da iyali. Jajircewar AREWA24 wajen samar da shirye-shirye da harshen Hausa ya cike wani gibi ga masu amfani da harshen Hausa a duk fadin duniya, wadanda yawancinsu suke kama tashar AREWA24 ta hanyar yanar gizo domin saduwa da abokansu da 'yan uwansu. Ana dora shirye-shiryen AREWA24 a youtube.com/AREWA24channel kowane sati, kuma tashar tana karuwa da yadda ma'abutanta suke yawan kallonta a sauran kafafen sada zumunta na yanar gizo a AREWA24.com, facebook.com/AREWA24, Instagram.com/AREWA24channel, da twitter.com/AREWA24channel. AREWA24 tana tauraron Dan-Adam na EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000 da kuma ACTV distribution platform. Abokan huldar AREWA24 sun hada da Jordan Media City, Eutelsat and Globecast.

Domin neman Karin bayani ku tuntube mu a: info@arewa24.com.